"Yanzu kinfison inda zakije a maidaki kaman baiwa?...baki da gatan komai sai yanda akayi dake?... Dija njasan bani da ko sisi amma ban barin wani ko wata ta wulankanta Mani Ku....yanzu tambaya daya nakeson yi maki...kin fison zama dxa wasu kanmu?...." Da Sauri dija ta girgiza mata kai,
"To wane dalili ne yasa kike kuka don NA hanaki zuwa aikatau?..." Ammi ta sake tambayan ta, tana shessheka ta fara cewa
"Ammi....Kawai inason mu dinga samu kaman yanda su hase ke samu..."
"Kinsan halin da take ciki?..." Bata idaba dija ta katseta dacewa
"Ammi babu halin da take ciki..kalli yanda ta koma ranar da ta dawo...Kuma tace min har boko take zuwa...nidai ammi ki bari in je...in babu dadi zan dawo..." Tafada da gaske, ammi.zama tayi tana kallon ta cike da mamakin yanda take magana babu alaman tsoro, kara fashewa tayi da kuka tana cewa
"Dan Allah ammi ki bari inje...in da akwai matsala zan dawo...Kuma ni wallahi inason boko..." Ta fada cikin kuka,
Ammi tsaya kallon ta kawai tayi saida tayi kukan mai isanta Sannan ammi tace
"Amma kinsan cewa ba ni kadai ke da iko da Ku ba ko?.... Dukda yan uwan ubanku basu damu da Ku ba nasan da zaran wani abu ya faru zasu samu bakin magana..." Da Sauri dija tace
"Ai duk suna birni...kawu nanu Kawai ne nan...ammi muje mu fada mashi...." Ta fada har jikinta NA rawa,
"Badai yanzu kike nufi bako?..." Ammi ta tambayeta, sadda kanta kasa tayi Sannan tace
"yanzu.." Tafada tana murmushi,
"Jaira... Babu inda zamu yanzu ..saidai gobe..in bai yarda ba sai ki hakura..." Inji ammi,
"Nasan zai yarda...ai ba damuwa yayi da rayuwata ba...." Tafada cikin jindadi,  hararanta ammi tayi Sannan tace
"Je kiyi salla...nasan rabonki da salla tun NA zuhr..." Bata idaba dija tace
"Ai har yanzu ban gama ba..."
"Amma kaman kinyi salla da zuhr
" aa NA duba naga har lokacin bai tsaya ba balle inyi wanka..."$ ta amsa mata kaman ba ita bace ke kwance kasa tana kuka kaman wata yar karama yarinya.
"Je ki kara dubawa..." ammi ta fada mata, da Sauri ta mike ta fita.

Yazid NA zaune kan gado babu kaya jikinshi kafafunshi cikin blanket waya ne hannun shi yana magana kaman mai jin bacci idanuwanshi lumshe,
"Baby I can't wait..." Ya fada cikin whisper, daga Chan bangaren mufi dake kwance sanye da kayan bacci ta danyi Dariya tare dacewa
"Can't wait for what?.." Ta tambayeshi, shima murmushi yayi yana kallon erection dinshi yace
"Nothing.. Kawai am eager to be with you.... Gani nake kaman 24 days din nan tamkar 24 months or year..." Idanuwa itama mufi ta lumshe saboda maganar shi ke yawo straight into her system, mika tayi Sannan tace
"Nikam kaman gobe nake ganin 24 days..." Yazid Dan kwantawa yayi yana cewa
"Don baki damu dani kaman yanda NA damu da ke ba...amma ni I feel rike in tariyo time din..."
"Don't worry... Kaman gobe ne..." Ta fada mashi cikin sanyin murya,
"Hmmm alright... I have been patient for a while.. So 24 days won't matter..." Ya fada ahankali,
"That's my love... Shiyasa nake kara sonka....$" Dariya yayi
"Da gaske?  Tell me why..." Yafada cikin whisper,
"Cos you are gentle..." Dariyan kasan makoshi yayi
"Hmmm baby am not that gentle... I don't want to disappoint you... On our first night..." Ya fada kasa2 yanda ki NA kusa dashi bazaiji abinda yake cewa, kuka karya mufi ta farayi tana cewa
"Ka bar fadan hakan...kana tadamin hankali..." Dariya yayi
"Name...Kawai am telling you kar ki daukine gentle don I might be bad ass..."
"I know you are not..."
"To shikenan...I will try to be gentle as I look..." Yayi assuring dinta, hira suka cigaba dayi for sometime Sannan sukayi sallama, Ahankali ya ajiye wayan, ana kallon joystick dinshi, tunani yake wai haka maza ke ji in suna magana da mata ko matsala gareshi din mostly in har zasuyi waya yana jin muryanta cikin kunnenshi sai ya samu erection, shidai gurinshi yayi aure ko ya huta da wannan matsalan.
Ahankali ya mike ya shiga bathroom ya sakar wa kanshi ruwa Sannan ya dawo ya shiga blanket ya rufe kanshi from head to toe.

The following day tun da wuri dija ta addabi ammi suka kama hanyan gidan kanin marigayin babanta wato kawo nanu
 Sallama sukayi ita da ammi suka shiga ba tare da an wani amsa masu ba don ana ganin kaman roko ya kawo su kaman yanda suke zuwa wasu lokuttan in abubuwa suka kakare masu, mutumin dake zaune yana wanke bakinshi da asuwaki ya kallesu
"lafiya tun dugudugu?..." Mutumin ya tambayesu, dija data nufi wurin shi tace
"lafiya lau...INA kwana..." Ta gaidashi tana durkusawa,
"Lafiya..." Ya amsa mata atakaice, ita ammi dakunan Matan gidan ta shiga tana gaidasu suna amsa mata atakaice wata ma Bata amsa ba Sannan ta nufi inda dija ke tsaye gefen kawunta, itama durkusawa tayi ta gaida nanu dake yi mata kallon wulakanci Kuma ba komai ya haddasa hakan ba illa yaso ya aureta bayan mutuwan babansu dija amma taki sai ya tsaneta
"Lafiya...wai me akayi ne?.." Ya tambayeta yana goge hakoranshi, ahankali ammi ta fara fadamashi abinda ke tafe dasu, sai da ta kai karshe Sannan ya kalli dija dake tsaye tana sauraron su

"Ke haka ne?..." Ya tambayeta
"Eh kawu..." Ta amsa mashi cikin sanyin murya
"To shikenan.. Allah ya bada saa..." Ya fadawa dija don ko kadan bayason magana da ammi,
"Yauwa kawu Ameen...mun gode.,.." Ta fada cikin murna sosai Wanda ko kadan Bata Iya boyewa,
"Ammi mu tafi..." Ta fada tana barin wurin da Sauri, itama ammi ta bi bayanta tana tafiya ahankali kawu nanu ya bi bayanta da kallo yana cewa
"Ga mace har mace amma ta bar dukiyanta suna wulakanta babu mai kula dasu...yanzu da ina nan ina morewa amma ta yi min bakin ciki..." Ya fada tare da Jan tsoki, ammi fita tayi Bata kar bin ta kan Matan gidan ba don su har yanzu kishi sukeji suna ganin kaman tana iya amincewa mijin su ya aureta don ta fisu komai da komai,
 Dija NA tsaye waje tana jiran fitowan ammi tana fitowa dija tayi saurin cewa.
"Ammi ki bani kudin abun hawa in tafi daura in fada mata kun amince..." Hararanta ammi tayi ta wuceta Bata tanka mata ba, har suka kai.gida dija Bata bar fada mata ta Bata kudi ta tafi daura ba, saida ammi taga zata sha mata kai Sannan ta fada mata Hajiya Aisha zata dawo anjuma, sai lokacin dija ta sake ta fita ta fara gayawa kawayenta zata birni, da sun tambayeta katsina zata? Sai tace
"Kambu ni na wuce katsina.. Kano zani..." Duk saida tabi kusan dukkan gidajen kauyen su ta fada masu zata birni
 Ammi kam tunanin yanda dija Bata damu dasu ba Kawai take don ko kadan ta nuna bazatyi missing dinsu ba, sai kuma ta tuna da yarinta ke damunta. Dija wanke faded clothes dinta tayi ta shanya su ko abinci bataci ba, ammi kallonta tayi
"Ke baki ma tunanin halin da zamu shiga in kin tafi...kinsan bamu da komai gidan nan..Kuma da tallan nan muke ci, gashi zaki tafi..." Dija Dan Bata rai tayi Sannan tace
"ammi ki bawa binto ta saida mana..." Hararanta ammi tayi
"Amma baki da hankali... Wannan yarinyan zan bawa tallan fura?..."
"Yo ammi ni ai ban kai ta ba NA fara tallan awara..to ki yi mata awara ta dinga kaiwa tasha...." Ta fada in  I don't care manner, ji take kaman ta kira Hajiyan ta zo ta dauketa.
Sai bayan sallan asar Hajiya Aisha tazo, alokacin kam dija har ta fidda ranta zatazo ita Kuma ammi tana ta aduan Allah yasa kar tazo sai gata da sallama ta shiga cikin gidan da gudu dija ta rungume ta tana cewa
"Sun yarda..sun yarda..." Ta dinga fada tana rike da Matan, itama Hajiyan riketa tayi tana cewa
"Da gaske?..." Kai akwai dija ke ta daga mata cikin jindadi, Hajiya kam tamkar Tasan halin da suke ciki, kallon ammi dake zaune tana murmushi tana aduan Allah yasa aso yarta tamkar yanda Hajiya Aisha ke son dija.
"Kisa yara su biyoni..." Ta fada mata tana fita, da Sauri su dija da sauran yan gidan suka bi bayanta, bayan motanta ta bude sai ga shinkafa da mai da magi sai su taliya katon da macaroni. Ihu su dija suka fara Sannan suka fara shigowa da kayan da Sauri ammi ta mike tsaye tana kallon su. Nan ta zube kasa tana godewa Hajiya Aisha.
Bayan sun zauna ammi take shaida mata sun yarda ta tafi da dija
"don Allah kisa a kula daita...Dan Allah kisa su dauketa tamkar su suka haifeta..." Inji ammi dake hawaye, kafadarta Hajiya ta dafa Sannan tace
" ki kwantar da hankalin ki...yaran da na kai gidan aikatau sunfi su ashirin Kuma baa taba samu

matsala ba...kullum iyayensu cikin gode min suke saboda yanda rayuwan yaransu ya chanza...don haka ki kwantar da hankalin ki..." Kai ammi ta gyada mata. Sannan suka tashi tafiya dija ta dauko old Ghana most go dinta, Dariya Hajiya tayi tana cewa
"Ki bude wannan bag din in gani..." Dan dija ta baje kayanta, banda Dariya babu abinda Hajiya takeyi,
"Kawai ki bar wayan nan..in munje daura sai in Dan samo maki.kaya kafin in kaiki..." Tsalle Kawai tayi ta fita ta tsaya jikin motan tana kallon yan kauyen su da suka taru jikin motan suna kallon ta, Hajiya fitowa tayi ta bude motan dija ta shiga Sannan suka tafi.
[3:14PM, 3/20/2018] 鈥�+234 806 125 0020鈥�: 鋏ゐ煉氿煉滒熯ゐ煉橀煉�
NA CUCE TA
馃挧馃拞馃挍馃柮馃挌鋏�

庐zuwairat(ummu Maryam

6鈧�

Dija ko kallon mutanen batayiba balle ta daga masu hannu kaman yanda suke daga mata hannu, ammi dake kuka Kawai take kallo tana tausaya mata amma in ta tuna yanzu basu da matsalan abinci sai ta samu nutsuwa, har suka iso cikin garin daura Bata ce uffan ba, Hajiya kallon ta tayi taga yanda tayi sanyi farat daya ta saki murmushi tare dacewa
"Lafiya dai ko?..." Ta tambayeta cikin muryan dake kwantar da hankalin mai sauraro, dija daga idanuwa tayi ta kalleta
"Babu komai..." Ta fada muryan ta NA rawa, tunanin yanda komai zai kasance Kawai take, tunda take Bata taba kwana wani wajen ba sai in sun je kauyen ammi.dake bauchi shima tare suke zuwa Kuma su dawo tare, Kawai sai taji Kuma batason tafiyan. Ana kiran magrib suka shiga gidan Hajiya tayi parking motanta suka fito daidai lokacin da wasu yanmata biyu suka fito daga falonta, daya babba ce sai daya kaman dija, dukkan su sanye da kaya ta alfarma, dija kallon su tayi ta fara tunanin ya akayi ita bata tura yaranta aikatau ba sai ta tuna Ashe su masu kudi ne Kuma ita talakace, gaidasu tayi suka shiga cikin falon. Jikinta sai rawa yake don she feels so out of place, yanmatan sai kallon ta kawai suke, Hajiya zama tayi ta dauki wayanta ta kira number yayan Hajiya karama ta shaida mata ta samu yar aikin da suke bukata Kuma ta fada mata zata shigo mata daita gobe.

"To shikenan.. Allah ya kaimu.." Inji yayar Hajiya karama. Sallama sukayi Sannan Hajiya Aisha ta kalli yarta dake zaune kusa daita tana kallon dija
"BaBy zaki aramin kayanki biyu...zuba uku..." Yarinya Bata rai tayi
"Mom me zakiyi da kayana Kuma?..."
"Zan Bata ne....I promise zan saya maki replacement..." Sai alokacin yarinya ta saki fuskarta, kallon dija data sadda kai kasa tayi Sannan ta kwalawa nata mai aikin kira, nan wata babban budurwa ta fito, dija kallon ta tayi
"Tabdin...wallahi bai kaiwa kaman wannan, ina yar aiki..." Ta fada cikin ranta, y
Mai aikin durkusawa tayi ta gaida Hajiya ta amsa Sannan Hajiya tace
"Ki kaita dakinki..ki Bata abinci taci ta koshi Sannan Dan Allah ki duba kanta in yana bukanta gyara ki wanke mata kisata ta wanke bakinta ta wanke koina NA jikinta zan kawo kaya yanzu....." Hajiya ta fadawa mai aikinta,
"To ..." Kawai yarinya tace Sannan tayiwa dija alaman tazo, da Sauri ta mike ta nufi wajen yarinyan sukayi dakinta, dija bude bakinta tayi tana kallon dakin mai aikin,
"Kam Allah kasa nima a bani kaman quartan wannan dakin Dana haye..." Ta fada cikin ranta.
"Ki zauna..." Yarinyan ta fada mata tare da nuna mata katifan dake kasa, da Sauri dija ta zauna ita Kuma ta fita daga dakin, few minutes later ta dawo da jelof din taliya dayasha kayan miya,
"Wow dadi...Allah yasa inda zaa kaini su dinga cin irin wannan..." Ta saki fada cikin ranta tana aman abun daga hannun ta, nan dija ta apkawa abincin ta cinye tas ta tside kwano Sannan ta ajiye, yarinyan dauke kwanon tayi ta kai kitchen Sannan ta dawo,
"Bude kanki in gani..." Yarinyan ta fadawa dija, da Sauri dija ta bude kanta, kitson kanta yafi wata daya dayi Sannan kanta dilindilin,
"Kambu..da akwai aiki..." Inji mai aikin Hajiya Aisha,
Da Sauri ta fita daga dakin ta fadawa Hajiya Aisha status din kan dija,
"Kina da sauran relaxer?..." Hajiya ta tambayeta,
"Eh ..."
"To ki shafa mata kan..don gaskiya bazan kaita a haka ba tunda manyan mutane ne..." Ta fada, nan mai aikin ta koma ta bawa dija tsinke ta shigar daita bathroom dinta
"Ki tsaya nan ki kwance kanki..in kin gama kiyi min magana..." Ta fada mata Sannan ta fita ta barta nan tsaye, dija kam tsaya kallon bathroom din tayi tana gani ya ninka dakin su kyau sau goma, dukda babu wasu kayan wanka cikin bathroom din amma tiles din wurin Kawai ya isheta kallo, da Sauri ta kwance kanta dake gari bisa jikinta daman Zane ne guda six amma ki tsaganta baka ganin saboda tsufa. Lekawa tayi ta kalli mai aikin
"NA gama..." Ta fada mata, budurwa mikewa tayi ta dauki sauran relaxer ta shiga bathroom din, nan ta umarceta data durkusa Sannan ta fara shafa mata, tana shafa wa tana mamakin irin gashin dija, don Bata San dunkule yake ba saida ta fara shafa man, tafi minti talatin tana shafa mata,
"Lallai.. Kina da tsawon gashi..." Ta fada, dija dake neman kuka saboda zafin relaxer tace
"Yanke min ammi take saboda tsawo..." Ta amsa mata muryan ta na rawa, few minutes da gamawa dija ta fara yarfe hannuwanta tana cewa
"Ki cireshi haka nan...wallahi zafi nake ji..." Yanda tayi maganan yasa ta Dariya, nan ta wanke mata kai tas taga yanda kanta ke silky saboda baki da tsawo,.
"Hmm daman mu yan kauye munfi yan birni komai.. Amma wahala bai sa a gane hakan..." Yar

aikin Hajiya Aisha ta fada cikin ranta, saida ta gama ta hada mata ruwan wanka mai dumi, dija kam jinta take kaman princess,
"Ni ake hadawa ruwan wanka mai dumi..." gari su kam duk sanyi sai dai kayi wank da ruwan sanyi din baka samun ruwan.
"Ki wanke jkinki sau biyar kafin ki fito...kinji?..." Da Sauri dija ta gyada mata kai. Tana fita dija ta cire wet clothes dinta ta fara dirje jikinta kaman mai dilka da sabulu mai kamshi don ita dadin sabulun Kawai take ji, sai adua take Allah yasa da akwai irin wannan hutun inda zaa kaita. Wanke jikinta tayi sosai har in ta saka ruwa jikinta bai zama saboda yanda ta wanke kanta. tsayawa tayi tana kallon kanta kaman yanda ta saba, tafi hour tsaye har saida taji an Dan buga kofan bathroom din Sannan tayi saurin cewa
" na gama....kayanane suka jike..." Ta fada da karfi,
"Ki daura wannan tawul ki fito..." Ta fada mata, dija tsaya kalle2 tayi tana mamakin meye tawul, jin shuru yasa mai aikin cewa
"Wannan farun kyallen zaki daura...." Sai lokacin dija ta gane ta dauko towel ta daura amma sai ta kasa fitowa saboda yanda bai da tsawo,
"Na daura...." Ta fada, kanta kasa sai gasjinta baje kan shoulder ta, budewa mai aikin tayi ta shigo ta zuba mata makilin a brush ta bata ta nuna mata yanda zatayi dashi.
Atakaice nan take dija ta fito kal kaman ba itaba, Hajiya ta shigo mata da wata doguwar Riga yarta ta Bata, ita kanta hajiya sai da ta tsaya tana kallon gashin dija don ba karamin mamaki tayi ba.
Kallon mai aikinta tayi Sannan tace
"Dan Allah ki Bata shawaran da kike bawa sauran in an kawosu kafin In akaisu gidan aikin su..." Inji Hajiya Aisha,
"to..." Ta amsa mata, fita Hajiya tayi dija ta zumbula rigan da aka bata, nan mai aikin Hajiya Aisha ta fara cewa
"Kina jina?..." da Sauri dija ta gyada mata kai,
"NA farko inda zaa kaiki ba gidan Ku bane...gidan aikinki ne...ki tabbatar kina girmama koda akuyan gidan..." Da Sauri dija ta kalleta, itama kallon ta tayi
"Eh din...dole ki girmama su...babu ruwan ki da abinda baa saki ba...duk abinda akace kiyi kiyi...in ance ki bari ki Bari...banda kwadayi...banda zuwa inda baa ce kije ba...banda shisshigi...banda yayata sirrin uwar dakinki ko na wata...babu ruwanki...banda sata..." Again dija kara kallon ta tayi
"Yo kina mamaki ne?.... To da akwai wata yarinya da Hajiya ta kai saida aka maidota wai tana dauk2....don haka ko kudin su zai dinga yawo kasa babu ruwanki don wani lokacin gwadaki suke...kar kiga babu mai kallonki kiyi abinda baace kiyiba...kiji tsoron Allah a duk inda kike...Kuma kar zaman birni yayi maki dadi ki mance inda kika fito...kinji ko?..." Da Sauri dija ta daga mata kai,
"Sannan babu mai son yar aiki kazama...kiyi wankan ki kafin ki fara aikin gida....don haka ki tabbatar kina mikewa da wuri...ki kula da kanki...Kuma in kina da wata matsala ki fadawa uwar dakinki... Mussanman irin matsalan mu na mata...da fatan kinji abinda nake fada maki...." Da Sauri dija ta kara daga mata kai
"Ke ki bar daga kai.kaman wata kadangaruwa...ki dinga amsawa..."
"To ..." Dija ta fada, wasu advice ta Kara Bata sosai kan yanda zata zauna da su batare data

samu wata matsala ba, dija taji dadi sosai don sai gata tana cewa
"Nagode..." Labari suka cigaba dayi har bacci ya dauki yar aikin Hajiya Aisha ita kam dija yanda ta ga rana haka ta ga dare. Tun da asuba mai aikin Aisha ta tashi tayi wanka itama dija tayi wanka ta maida kayan ta bi bayanta suka fara aiki tana nuna mata abubuwan daya kamata mutum yayi,
"Ai Kwara wannan da dakan fura..." Ta fada cikin ranta,. Kafin bakwai da rabi sun gama komai har mai aikin Aisha ta kusa ida breakfast. Sai karfe takwas Hajiya ta fito ta sha tea da bread su Kuma yaranta sukaci abincin, mai aikinta ta debo abinci ta kai dakinta sukaci da dija Sannan Hajiya Aisha ta kirata ta fito, wata karamar jaka ta bata
"Gashi da akwai kaya kala uku cikin shi...ki kula dasu kafin su kara maki wasu..." Da Sauri dija ta amsa Sannan suka kama hanyan katsina. Gidan yayar Hajiya karama suka isa, nan ma dija baki ta bude don kyau da girman gidan, matar dake kaman daya da Hajiya karama ta kallesu fuskan ta dauke da murmushi tana cewa
"Wannan yarinyan tana da kyau.. Ina kika sameta?..." Ta tambayi Hajiya Aisha, Dariya Hajiya Aisha tayi ta labarta mata yanda akayi ta samu dija,
"To alhamdulillah... Yanzu bari in baki address dinsu dukda gidansu ba boyayye bane a garin Kano..." Nan ta rubuta mata address, ta mika mata, Sannan tace
"Bari in dauko maki NA mai..." ta fada tana hayewa upstairs, dija dai kanta kasa gabanta ne Kawai ke faduwa saboda tsoro, few minutes later ta sauko da bandir din Dari biyu ta Bata,
"Wannan ai yayi yawa..." Inji Aisha, Dariya tayi
"Inafa...ai kinyi kokari...ki gaida manasu dukda muna da biki nan gidan..."
"Kanwar taki ce zata aurar?.." Kai ta girgiza mata
"Dan abokiyar zamanta ne zaiyi aure ...." Ta fada mata
"To Allah yasa ayi a saa... Bari mu tafi tunda muna da tafiya gaban mu..." Ta fada tana jefa kudin cikin bag dinta tare da mikewa. Nan sukayi sallama Sannan suka kama hanyan Kano
[3:14PM, 3/20/2018] 鈥�+234 806 125 0020鈥�: 馃拰馃挌馃挍馃枤鉂ゐ煉�
NA CUCE TA
馃拰馃挌馃挍馃枤馃挅鉂�

庐zuwairat(ummu Maryam)

7鉃�

Ko uffan dija batace ba har suka iso garin Kano,Hajiya kallon ta tayi ta fara Bata new advice har suka iso kofar wata katuwar gate, gaban dija kara faduwa yayi ta Dan leko da kanta tana kallon gate din da Hajiya ke horn a bakinta, wani ne ya leko ya kalli motan yaga mace ce da wata yarinya ya koma ciki Sannan ya bude gate din don ba kowa ake bari ya shiga gidan ba saboda tsaro, ahankali Hajiya shiga gidan itama tana mamakin girman gidan,
"Hmm gaba da gabanta..." Ta fada cikin ranta, ahankali tayi parking motanta a available space dake wurin ta fito tana kalle2, fadin girma da haduwan gidan is a waste of time amma ko motocin gidan Kawai are enough, Manyan gidaje six ke da akwai wurin, hakan yasa Hajiya Aisha ta rasa inda zata shiga, dija kam boyewa tayi bayan Hajiya tana kallon gidan, mai gadi me ya nufota da murmushi fuskan shi, gaidata yayi ta amsa sannan Hajiya tace
"Dan Allah bangaren Matan gidan zakanuna min..."
"Wacce daga cikin su?.." Mutumin ya tambayeta
"Karama matar..." Ta amsa mashi, nuna mata gidan dake middle yayi yace
"Nan ne..." Ya fada mata Sannan ya kokma duty post dinshi su Hajiya suka nufi inda aka nuna mata, ita kanta Hajiya Tasan tunda take kai yara gidan aiki Bata taba zuwa gidan da yayi Rabin wannan ba wajen girma da kyau, dija kam tafiya take amma tamkar an rike mata kafa, ahankali ta dinga takawa tana kare kanta da Hajiya Aisha dake gabanta, bakin kofan ta Hajiya ta tsaya ta danna wata bell, few minutes later wata budurwa ta bude ta gaidasu, amsawa Hajiya tayi Sannan tace
"Hajiya tana ciki?..."
"Eh...Ku shigo..." Yarinyan ta fada masu tana komawa gefe, cikin falon suka shiga sanyin ac ya bugi dija nan take taji kaman tana fever, tafiya ta dingayi a hankali don kar tiles ya kwaceta, Hajiya zama tayi dija ta zauna kasa kanta kasa heartbeat dinta NA kara highing by the minutes, Hajiya kam baki ta bude tana kallon ikon Allah tana mamakin yanda aka tara abun duniya waje daya, budurwan data bude kofan ce ta kawo drink da wasu elegant cups biyu ta ajiye Sannan tace
"Bari in kirawo ta...." Ta fada tana barin wurin, Hajiya kallon dija tayi
"Dija kinyi saa... Ban taba kai yarinya irin wannan gidan ba...sai kiyi ladabi ki bi doka ki ci arziki...." Ta fada mata kasa2 tana tsoron kar CCTV ya dauki maganar ta don tasan baa rasa sawa cikin irin wannan gidan. Bayan minti kaman biyar Yarinyan ta dawo tace
"Gatanan zuwa..." Ta fada masu Sannan ta bar falon. Sunfi minti goma shabiyar zaune Sannan Hajiya karama ta fito da faraa fuskan ta, gaisawa sukayi Sannan Hajiya karama tace
"Kece Hajiya Aisha?.." Ta tambaya
"Eh nice...Kuma wannan itace Yarinyan da kikace a samo maki...." Ta fada tana nuna dija dake lankwashe kasa, sai lokacin dija ta gaidata muryanta na rawa
Hajiya karama kura mata ido tayi tana kallon ta Kuma tana mamakin kyauwunta,
"Lafiya lau..Wallahi I thought she's your daughter... Ah ina kika samo wannan beauty..." Tafada cikin raha kaman sun Dade da sanin juna da Hajiya Aisha, Dariya kawai tayi , Hajiya karama kallon yanda dija ke nonnokewa Kawai tayi ta saki Dariya
"Ya sunanki?..." Ta tambayi dija
"Kha...fi...ja..." Ta fada kanta kasa don ko sau daya Bata daga kai ba,
"Ah...ah...ah....sunan hajiyar mu gareki Ashe...kice NA samu sabuwar uwa...." Tafada cikin Dariya, itama Hajiya Aisha Dariya tayi hankalin ta kwance da Hajiya karama Bata nuna batason

dija ba,
"Asabe!... " ta kwala kira, sai ga yarinya data bude masu kofa ta dawo ta durkusa gaban Hajiya karama,
"Ga sabuwar mai taimaka maki an kawo...ki.tafi da ita dakinki..." Ta umarceta, Dariya jin dadi budurwa da bazata wuce shekara sha takwas ba tayi tana nuna jin dadinta karara da samun mai rage mata aiki,
"Taso..." Ta fadawa dija, ahankali dija ta mike jikinta na rawa, sai lokacin ta daga kai ta kalli Hajiya Aisha Kawai sai ta fara hawaye, don Kawai sai taji gidansu take so,
"Ah...ki bar kuka...nan ma gidanku ne kinji?.." Hajiya karama ta fadawa dija, da Sauri dija ta hadiye kukan ta fara takawa ahankali tana bin bayan asabe, Hajiya karama kallon ta kawai take don kallon yar gidan manya kawai take mata don ko kadan Bata kama da yar talakawa, saida suka bar falon Hajiya karama ta kalli Hajiya Aisha
"Amma wannan yarinyan zata Iya aiki kuwa?... Naga she's a little bit dull..." Dariya Hajiya Aisha tayi Sannan tace
"Sosai kam Hajiya...Kawai yanzu kunya take ji..amma ina tabbatar maki.babu abinda bazata iyaba..."
"To shikenan.. Nawa ake biyan yaran da kike kaiwa gidan aiki?..." Hajiya karama ta tambaya, murmushi Hajiya Aisha tayi tace
"Ai duk yanda kika bada daidai ne..."
"To shikenan...masu aikin mu dubu talatin ake basu duk wata ga baki dayansu don haka zaa din biyanta...." Wani irin dadi Hajiya Aisha taji don tunda take kai yara gidan aiki babu inda ake biyan dubu ashirin balle talatin
"To shikenan... Hakan yayi sosai...." Inji Hajiya Aisha,
"To sai ki bada account number in bada a bawa manager kar a manta da albashinta..." Da Sauri Hajiya Aisha ta dauko Biro da  paper ta rubuta ta mikawa Hajiya karama Sannan tace
"Ina yaran ne?.." Ta tambayeta
"Suna chan bangaren babban mominsu....bari in sa a hada maki wani abu naci...." Inji Hajiya karama,
"Na gode kwarai... Tafiya zanyi don inason in shiga kasuwa kafin in koma katsina...."
"Haba da wuri haka?... Haba ki bari sau gobe mana..." Injin Hajiya karama,
" sai in NA sake dawowa in Allah ya yarda..." Ta fada tana mikewa,
"Ina zuwa..." Hajiya karama ta fada mata Sannan ta bar falon bayan yan mintuna goma tadawo da wata katuwar Leda dauke da manyan atampa guda uku sai perfumes, sai kudi cikin envelope
"Gashi a rabAwa yan gida..." Hajiya karama ta fada tana mika mata ledan
 "Har da wata hidima?... Gaskiya NA gode...Allah ya aka da alkhairi... Allah ya kara girma...nagode kwarai..." Ta fada cikin jindadi,
"Babu komai... Bari muje in kaiki gurin uwargidata Ku gaisa kafin ki wuce..." Hajiya karama ta fada tana shige mata gaba, bayanta Hajiya Aisha tabi har falon da yaran gidan ke wasa ita Kuma Hajiya babba zaune kan kujerana alfarma tana kallo zee aflam, da sallama suka shiga Hajiya karama ta shaidamata an kawo mai aikin. NaN suna gaisa Sannan Hajiya Aisha ta tafi bayan itama Hajiya babba ta Bata atampa da turare.

Dija baki ta bude tana tafiya ahankali tana waige2 har asabe ta bude dakinta suka shiga, dija tsayawa tayi tana kallon ikon rabbi don dakinta katuwa ne Sannan ga katon gadon da ko amaryan garinsu Bata isa ta mallakesu ba,
"Ki zauna mana..." Asabe ta fada mata amma dija bataji ba saboda yanda take kallon ceiling din dakin, kallon katon madubin dake jikin bango tayi ta tsaya tana kallon kanta, sai yanzu ta gan kanta sosai yanda take so, kallon kayan shafan dake kan mirror tayi ta dauke kanta ta kalli wata katuwar bag dake dakin
"Ki zauna mana.." Asabe ta fada tana Dariya,sai lokacin dija ra dawo hayyacinta ta kalli asabe dake dariya, sauke kanta kasa tayi tana murmushi,
"Ya sunanki?..." Ta tambayeta sounding friendly.
"Di...ja...." Ta amsa mata,
"Ni sunana asabe...sannunki da zuwa yaruwa...daga wane gari kike?..." Ta tambayeta,
"Baude...." Dariya asabe tayi
"Inane Baude?...." Dija dai shuru tayi don batasan abinda zata fada mata ba
"Ni yar dala ce...shekaranki nawa?..." Asabe ta sake tambayanta, shuru dija tayi kaman mai tunani Sannan tace
"Sha uku ko hudu..." Idanauwa asabe ta zaro
"Shine kike da tsawo haka?...wallahi nayi tunanin shekarunmu daya...Ashe ke yarinya ce...bari in dauko maki abinci...." Ta fada Sannan ta mike, fita tayi daga dakin dija ta kara mikewa ta nufi wajen split air conditioner, sai kallon abun take hannun ta ta kai wajen taji wani irin sanyi NA ratsa hannun ta, da Sauri ta dauke hannun ta takoma ta zauna har lokacin bata bar kalle2 ba. Rice and stew cike da kifi asabe ta shigo dashi ta ajiyewa dija sai ta bude Dan karamin fridge dake dakin ta dauko ruwa ta ajiye mata
"Bisimillah...." Asabe ta fada mata, da Sauri dija ta sauko kasa ta zauna ta fara cin abincin tana kara godewa Allah, daman dija Bata wasa da cikinta sai gata ta cinye abincin tas Sannan ta sha ruwa, asabe sai kallon ta tana murmushi don haka nan taji tana son dija. Sai da dija ta gama cin abincin Sannan asabe ta fara fada mata ayyukan da zasu dinga yi, itadai dija sauraron ta kawai take tana lumshe idanuwa saboda sanyin dake ratsata daman batayi bacci ba jiya
"Ko zakiyi bacci ne?.." asabe ta tambayeta da Sauri ta girgiza mata kai, Dariya asabe tayi
"In zakiyi bacci ki kwanta kafin..." Bata idaba wayanta ya fara ringing da Sauri tayi picking, shuru tayi tana saurаron abinda Hajiya karama ke fada mata
"To..." Ta amsa Sannan ta ajiye wayan ta kalli dija,
"Hajiya ta ce in kawoki bangaren Hajiya babba,..." Ta fada mata, da Sauri dija ta mike itama asabe ta mike suka fito zuwa part din Hajiya babba, sallama sukayi suka shiga kan dija kasa hannun ta rike da junansu duk yan yaran dake wasa Tare da yanmatan dake kallo kura mata ido sukayi. Durkusawa tayi ta gaidasu har da yanmatan, kallon juna sukayi suka tuntsure da Dariya suna kallonta with adorations, itama Hajiya Dariya take, rarrafawa tayi wajensu Hajiya ta kara gaidasu suka amsa suna Dariya
"Amma wannan yarinyan da abun Dariya take..." Inji Hajiya babba dake dariya, har lokacin dija na nan durkushe kasa itama asabe Dariya take, marzuq da Ameera ne suka ce
"Small mom wannan mai aikice?..." Ihsan ce ta buge masu baki, sukayi shuru don yana daga cikin tarbiyan yaran gidan basu raina maaikatansu,

"Ku koma..." Hajiya karama ta fada masu, sai lokacin dija ta mike suka koma part din Hajiya karama marzuq da Ameera NA biye dasu suna kallon dija kaman madubi don duk a masu aikin gidansu babu mai kyauwun ta, kitchen suka shiga tare dija ta bude baki, su Ameera NA biye dasu har cikin kitchen sai cewa tayi
"Tea zan sha...." Inji Ameera,Dariya asabe tayi tana cewa
"Sarauniyar shan tea..." Ta fadawa Ameera dake yar shekara 8 amma tana abu kaman yar shekara uku saboda sangarta, cup asabe ta dauko zata hada mata tea sai cewa tayi
"Bake zaki hadamin ba...ki bari ita ta hada min..." Ta fada tana nuna dija,
"To kinji da ke take..." Asabe ta fadawa dija, Dan matsawa dija tayi kusa da asabe Sannan tace
"Meye hakan?..." Ta fada cikin whisper, cup asabe ta mika mata, ta kaita ta zuba ruwa Sannan ta bude mata katon tin NA milk da Ovaltine, ta dauki spoon ta mikawa dija Sannan ta umarceta data hadasu cikin cup, yaran sai kallon su suke suna Dariya tana gamawa ta mikawa Ameera ta amsa Sannan suka bar kitchen din.

Hajiya Aisha NA fita ta duba envelope din da Hajiya karama ta Bata taga mint na Dari biyar, dadi taji tana cewa
"This is what am taking about..." Tafada cikin jindadi. Kasuwa ta shiga tayi sayayya tare da siyan wasu atampa yan 3k guda uku don ta kaiwa ammi
[3:15PM, 3/20/2018] 鈥�+234 806 125 0020鈥�: 馃拐鈥ゐ煉氿煐ゐ煉涴煉�
NA CUCE TA
馃挍馃拰馃搭馃枺馃拐鈥�

庐zuwairat( ummu Maryam)

8鈧�

Daga kitchen dinning area asabe ta kai ta Sannan dakin daukan baki sai dakin su Ameera don dakinta Kawai take gyarawa sauran yaran suke gyara wurin su da Kansu,
"Ba wani aiki ke da akwai da yawa ba...Kawai dai baa sin gani kazanta ko kadan ..." Asabe ta fada mata suna komawa dakinsu, dija dai sauraron ta kawai take don gurin ta dare yayi ta kwanta,

"Kiyi wanka mana kafin lokacin sallan magrib.. Bamu da girki yau don haka babu aikin da zamuyi saidai in Hajiya ta bukaci muyi mata wani abu..." Inji asabe,
"Ina zanyi wankan?..." Dija ra tambayi asabe cikin sanyin murya. Mikewa asabe tayi  ta bude kofan dake cikin dakin tace
"Taso ki  shiga...." Ta fada mata, ahankali dija ta mike ta shiga bathroom din tana kallon ikon Allah don babu abinda ta Iya amfani dashi a wurin tsaya kallon bathroom din, asabe jawo kofan ta farayi dija tayi Sauri rikewa
"Ban...Iya...ba..." Tafada muryan ta na rawa. Dariya asabe tayi Sannan ta shiga cikin bathroom din ta fara nuna mata amfanin shower da heater tare da bathtub, dija kura mata ido tayi Bata ko kaftawa har asabe ta gama Sannan tace
"Yanzu ki nuna min abubuwa dana koya maki..." Fada mata, nan itama dija  ta fada exactly abubuwan da ta fada mata, mamaki ne ya kama asabe cos she explained everything perfectly. Nan asabe ta fita ta barta tayi wankan sai lumshe idanuwa take saboda yanda take jin dadin kamshin sabulun wankan. Atakaice cikin kwana uku dija ta gane kan bangaren Hajiya karama, har da sunayen yan gidan gaba daya kaman yanda asabe ta fada mata Kuma ba karamin dadi take ji gidan ba don within that three days ta chanza cos ko fita batayi Kuma gashi da sun gama aiki kwanciya suke suyi bacci, yanzu kam dija ta bar tsayawa bathroom ta kalli kanta sai dai a gaban mirror dake dakin su amma sai in asabe Bata dakin sai ta tsaya ta kunshe towel dinta ta kalli jikinta da kanta tana kashewa kanta ido tana Dariya , yauma tana tsaye gaban katon mirror tana kallon kanta asabe ta shigo da plate din abinci, da Sauri dija ta gyara towel din tana kallon asabe, itama asabe kallon mamaki tayi mata,
"Me kikeyi haka?..." Asabe ta tambayeta cikin surprise, da Sauri dija tace
"Babu komai..."
"Kaman ya babu komai..."
"Aa... Kawai wanka NA fito....shine nake shafa mai...."  Tafada ahankali, asabe dai Bata kara cewa komai ba ra ajiye abincin suka fara ci,.

Yazed ne kwance yana bacci, alarm ne ya tadashi ya mike da Sauri tare da godiya ga Allah ya shiga bathroom yayi wanka Sannan ya fito daure da alwallah. Kaya ya saka yayi salla nan cikin dakin Sannan ya cire jallabiya dake jikinshi ya shirya cikin suit ya fashe kanshi da perfumes ya fito looking handsome than ever, kallon agogon hannun shi yayi yaga 6:15am
"I still have some time..." Yafadawa kanshi tare da fiddo wayanshi daga cikin aljihunshi, number Hajiya yayi dailing suka fara hira
"Son ka dawo haka nan mana...wai nan da abuja kake wannan abun kaman Wanda ke abroad?..." Dariya yayi
"Ai mom wahalan tuki nakeji...Kuma sauran sati daya hutuna..."
"To shikenan... An turo maka pic din gidan ?..."
"Yes mommy... It's beautiful... Amma nan abuja zaa kawota....".
Yafada yana naughty laugh
"Kaci gidanku...nan Kano zaa ajiyeta..." Turo baki yayi kaman yana gaban ta Sannan yace
"Mom NA....aikin fa?..."

"Ka dinga zuwa every weekend..." Idanuwa ya zaro, yayi shuru Kawai baice komai ba don kar Hajiya tace yana mata rashin kunya, haka suka gama hiran ya fita daga quarters din zuwa office.

Yau Hajiya Aisha ta koma gidansu dija din kai mata kayan data sayo mata, da sallama ta shiga cikin gidan, da Sauri ammi dake zaune ta rafka ban tagumi ta mike
"Ah..ah..Sannu da zuwa..." Inji ammi Tafada cikin murmushin karfin hali,
"Yauwa..." Sannan suka fara gaisawa, ledan Hajiya ta mikawa ammi
"Gashi inji uwar dakinki dija...." Ahankali ammi ta bude ledan Bata wani yi murna kan kayan ba,
"Ya dija take... Ina Iya zuwa ganinta?.." Ammi ta fada har jikinta NA rawa, murmushi Hajiya Aisha tayi
"Ki kwantar da hankalin ki..diyarki tana gidan Hutu...Kuma albashinta dubu ashirin..." Da Sauri ammi ta kalleta,
"Wane irin aikine zatayi da zaa Bata dubu ashirin cikin kwana talatin?.." Ammi ta fada cike da mamaki.
"Ai NA fada maki yarki tana gidan manyan mutane... Yanzu karshen watan nan zan sayo maki waya sai ki dinga waya da yarki..." Inji Hajiya Aisha, dadi ammi taji har cikin ranta.

_A week later_

Yau yazid zai dawo sai shirya kayan dadi ake kala2 kaman sarki zaizo gidan mussanman Hajiya karama duk wata in yazid zai zo gida weekend haka zata dinga hidima ko kadan Bata gajiya don tana ji dashi tamkar ita ta haifeshi shima bai wasa daita.

Dija NA tsaye gefen asabe dake yankawa mai dafa abinci cabbage cos ba su ke dafa abinci ba,
"Wai me akeyi naga anata dafa abinci kala2?.." Dija ta tambayi asabe cikin kunnenta,
"Babban Dan gidan ne zaizo..." Ta amsa mata, kai Kawai dija ta karkata, haka suka yi aiki har suka gaba aka cika dinning da abinci dija kam sai mamakin yawan kayan take don gani take ko mutane goma abincin yayi masu yawa
"Kilan ci gareshi..." Ta fada cikin ranta. Sai wajen 12 suka gama komai suka koma dakinsu. Kwanciya tayi tana tunanin ammi da kannenta don she missing them beyond words, da tana tunanin it won't matter amma she's so wrong she miss them so much, at times in suna cin abinci da asabe sai tace
"Inama su ammi suna nan..." Take fada cikin ranta.

Around two yazid ya shigo gidan cikin wata beautiful and expensive car, da gudu yaran gidan sukaje bakin gate, shima da Sauri ya fito ko parking baiyiba ya dauki Ameera hannun daya ya dauki marzuq da hannun daya, nishi ya farayi
"Wai ...me kukeci....duk kunyi adding weight..." Tafada yana nishi kaman Wanda ya dauki buhun cement. Sauke su yayi suna Dariya, hannun shi cikin nasu suka shiga part din Hajiya babba
Da gudu mimata da Zainab dake zaune falo suka nufoshi, bude masu hannuwanshi yayi yana

murmushi, rungume su yayi
"Nayi missing dinku...." Ta fada masu
"Yaya bakayi missing dinmu ba...jiya dakayi waya da big mommy baka nememu ba..." Inji Zainab dake turo baki, Dariya yayi Wanda ya kara bayyana handsomeness dinshi
"To in ni ban nemeku ba Ku bazaku kirani ba?..."
"Ai bamu dakudi..." Inji mimata, kai ya girgiza yana cewa.
"Baku da kudi amma kullum kuna online..." Yafada tare da kama hanyan mini falon dake wurin, nan ya hangi Hajiya babba da Hajiya karama zaune fuskan su dauke da murmushi, da Sauri ya karasa wurin su ya durkusa Sannan ya gaida su,
"Ji yanda ka wani koma...duk ka rame saboda rashin abincin kwarai..." Inji Hajiya karama, Dariya Kawai yayi Hajiya babba kam murmushi Kawai take tana kallon danta cikin so da kauna
"Ai gani yanzu sai ki bani mai dadi inci in yi adding weight kafin in koma...." Hararanshi Hajiya karama tayi tana cewa
"Kana zuwa kana maganar komawa...." Tafada kaman tana fushi, zama yayi kan hannun kujeran da take ya rungumota,
"Da wasa nake mommy...." Yafada yana manna mata kiss a cheek dinta, mikewa Hajiya karama tayi ta kama mashi hannu,
"Muje kaci abinci..." Tafada tana janshi, Dariya yayi yabi bayanta don in da sabo ya saba,
"Yaya ina sarabanmu?..." Marzuq ya tambayeshi,
"Ban sayo komai ba..Ku bari da yamma sai in kaiku eleganza,..." Tsalle yaran suka fara, suka fita Hajiya karama NA rike dashi kaman wani karamin yaro, gate aka bude motan shahid ya shigo, tun daga nesa ya hangi yazid da Hajiya karama, Dan karamin tsoki yaja yana cewa
"The fun killer is back..." Yafadawa kanshi yana parking motanshi, Fitowa yayi ya nufosu sanye da three quarters dake low waist a kugunshi, yazid tsayawa yayi yana kallon shi
"Yaya sannu da zuwa..." Ya fada mashi kanshi kasa, yazid bai amsa ba ya tsaya kallon dressing dinshi,
"Ki daga ina kake?..."
"Daga factory...". Kallon up and down yayi mashi
" ina Sharif?...." Ya sake tambayan shi, hannun shi Hajiya karama ta kara rikewa
"Ka rabu dashi ..muje kaci abinci.. Don't waste your precious time on those silly boys...." Ta fada mashi, kai kawai ya girgiza ya bi ta, shi Kuma shahid ya tabe baki ya nufi part dinshi da Sharif yana tafiya irin NA niggas wandonshi sai Neman kwalewa yake. Saida suka isa dinning Sannan ta saki hannun shi, zama yayi yana kallon jerin abincin
"Small mom ya zanyi da wannan abincin?..."
"Kaidai kaci Iya cinka ka bar sauran..." Ta fada tana dauko mashi ruwa daga cikin fridge dake wurin, ajiye mashi tayi Sannan ta bar wurin ta koma bangaren Hajiya babba.

Yazid zama yayi yana kallon abincin sai yaji ya koshi don ya rasa abinda zaici Kuma ko kadan baison bata mata rai, Ahankali ya bude warmer daya yacikaro da white rice ya diba kadan Sannan ya bude next warmer ya zuba thick stew dake ciki ya fara ci bayana ya debi dambun nama ya zuba akai, saida yaci ya koshi ya sha ruwa yayi relaxing nan yana waya da mufida. Kawai kaman daga sama sai yaga dija ta bude kofa ta fito asabe NA biye daita, Dan tsaya kallon ta yayi har saida muryan mufida ya dawo dashi hayyacinshi, itama daga idanuwanta tayi

ta kalleshi tayi Sauri durkusawa
"Ina kwana?..." Ta fada da Sauri, sai kuma tace
"Aa.. Ina yini..." Ta fada muryanta NA rawa, Dariya asabe tayi yazid kam zaro idanuwa tayi yana kallon ta har lokacin waya NA kunnenshi, hade rai yayi ya daga mata hannu, da Sauri ta mike ta koma ciki, itama asabe gaidashi tayi itama ya daga mata hannu ya cigaba da wayanshi
Saida ya gama ya zauna nan yana tunanin wacece wacce ta fito daga dakin masu aiki, zama yayi nan ko zata Kara fitowa. Dija kam da Sauri ta zauna kan gado kanta kasa,
"Wai ya akayi kika rude?...ko baki taba ganin mutum mai kyauwunshi ba?..." Asabe ta tambayeta, dija dai kasa magana tayi saboda abinda ya makale mata a wuya,
"Ko kin taba ganin shi?.." Ta sake tambayanta, da Sauri ta girgiza mata kai,
"Kinyi shuru..."
"Ba..bu...komai..." Ta amsa mata tana Dan kwantawa,
"Bazaki sha ruwan ba?... Tunda NA manta ba sa ruwa a fridge ba..." asabe ta fada mata don diban ruwa suje amma ganin yazid yasa ta dawo don wani irin faduwan gaba taji data ganshi Sannan ko daidaida minti daya Bata fatan kara haduwa dashi don yayi mata kwarjini da yawa
"Anjuma zansha...." Tafada tana kara lafewa kan gadon,
"Kije ki debo mana...ko so kike in debo maki?..." Da Sauri dija ta girgiza mata kai
"To ki tashi ki debo ruwan..." tafada tana bude fridge ta dauko roban da take zuba ruwa ciki ta ajiye ta mika mata, ahankali dija ta amsa ta mike tana tafiya ahankali ta nufi kofan ta bude gabanta na faduwa, tana budewa ya kara daga manyan idanunshi suka kara hada ido, da Sauri dija ta kara komawa ciki ta maida kofan ta rufe.
[3:16PM, 3/20/2018] 鈥�+234 806 125 0020鈥�: 馃拰馃挅馃挅馃拰馃挅鈥�
NA CUCE TA
馃拰馃挅馃挅馃拰馃挅鈥�

庐zuwairat( ummu Maryam)

9鈦�

Da Sauri asabe ta mike
"Lafiya?..." Ta tambayi dija da ta komo ciki kaman ta ga ghost,
"Ya...na... Nan....nidai tsoron shi nakeji...." Kallon mamaki tayi mata,
"Tsoro Kuma?... In kina haka kina Iya rasa aikinki...ya zaki dinga haka kaman kinga gawa?...shine fa babban gidan nan...in Hajiya taji tana iya koranki don Bata hadashi da kowa ba...yanzu kije ki debo ruwa kaman babu abinda ya faru kar ya fadawa Hajiya...." Asabe ta fada mata cikin fada, da Sauri tace

"To...." Tafada tana kara komawa bakin kofan, yazid kam zama yayi yana kallon ikon rabbi,
"What such of insanity is this?.." Ta tambayi kanshi, mamakin yanda take gwalo dukkan manyan idanuwanta in sun hada ido Kawai yake,
"Did she know me from somewhere?..." Ya sake tambayan kanshi, jin an kara bude kofan yasa ya kara maida hankalin shi ga kofan, dija ce ta fito wannan Karin Bata daga kai ba, Allah ya taimaketa da akwai distance tsakanin inda yake zaune da inda take, tunawa tayi da ya yana Iya fadawa Hajiya abinda tayi kaman yanda asabe ta fada mata, ahankali ta fara takawa kanta kasa, yazid kam kara balancing yayi yana kallon each and every step dinta yana mamakin yanda take tafiya kaman an somata cikin ruwa, kafanta sai rawa yake, Kawai sai ya tsinci kanshi da kallon waist dinta, dukda tana sanye da doguwar Riga yana ganin hip bone dinta, da Sauri ya kauda kanshi gefe har lokacin bai bar tunanin ina small mom ta samo wannan unique gal ba, dija NA jinta cikin kitchen ta saki ajiyan zuciya tare da dafa saitin heart dinta dake beating a very high rate, saida tayi rike sink din da zata debo ruwa for like ten minutes Sannan ta dawo normal, da Sauri yazid ya mike daya tuna baiyi sallan zuhr ba, barin falon yayi amma to his surprise he found himself turning back to look at the kitchen kafin ya bar falon. Direct ya wuce part dinshi NA gidan Wanda shi kadai ne gurin. Alwallah ya dauro ya fitoyayi salla ya zauna nan kan praying mat. Ko tunanin me yake oho. Yafi minti talatin zaune Sannan ya chanza kayan jikinshi zuwa English wear ya fita. Part din Hajiya babba ya tafi ya samesu nan ya shaida masu zaije factory wajen Abba sukayi mashi adawo lafiya , at that moment Kawai sai yaso ya tambayi Hajiya karama inda ya samo yarinya amma sai ya tuna da halin ta da saurin zargi da Kuma tambaya. Haka ya fita ya shiga motanshi ya nufi daya daga cikin factory din babanshi.
Dija na Gama deban ruwan ta fito ahankali tana aduan Allah yasa ya bar gurin Kuma luckily Bata tardashi ba, da Sauri ta shiga dakinsu ta maida kofa ta rufe, asabe kallon yanda tayi tsuru2 Kawai take, ajiye ruwan tayi cikin fridge Sannan ta koma ta zauna har ta tagumi,
"Wai meke damunki?.." Asabe ta tambayeta cikin kulawa, girgiza kai Kawai tayi alaman nothing,
"Ya zaayi ki ce babu komai alhalin cikin minti daya kika chanza...ki fadamin.. Kinga tamkar yaya nake a wajenki..." Tafada mata ahankali,
"Ni banason... wannan mutumin..." Ta fada cikin sanyin murya, maganar ta Dariya ya bawa asabe,
"Me yayi maki.daga ganinshi zakice bakison shi?..." Da Sauri dija tace
"Babu komai... Nidai...banason shi..." Tafada muryan ta na rawa, rike kunne asabe tayi
"Kinsan wallahi kar ki bari aji wannan maganan daga bakinki...haka nan zakice bakison shi... " dija dai shuru tayi tana tunanin how she feels about him the first instant, Kuma ita kanta Bata iya defining feeling dinta amma she's just calling it hate,
"Amma wayan nan biyun sunfi shi kirki..." Dariya Asabe tayi tana cewa
"Lallai bakisan kan abun ba...kina nufin shahid da Sharif sunfi shi kirki?... Kambu...to wallahi karkiyi fatan lambanki ya fito wajensu don har wanki mota sai su sakaki...Kuma suyi zaune suna kallon ka suna dariya....shi kam babu ruwan shi da kowa..mussanman mu maaikatansu..." Baki dija ta bude dataji ance wanki mota
"Kuma gabansu Hajiya suke kasaku wanki mota?..." Kai.asabe ta girgiza mata
"Aa.. In sun ga su Hajiya sun fita sai suce ni da haya... Muyi masu car wash....kaman yanda suke fada..."
"To meye maanan ka...was..." Dija ta tambayeta,

"Oho masu..." Dan Bata rai dija tayi Sannan tace
"Kilan yan iska ne..." Tafada Ahankali, da Sauri asabe ta kalleta,
"Ki bar furtan irin wannan maganar..babu kyau.." Kai dija ta gyada mata,
"Ki je kisha ruwan..ki kwantar da hankalin ki bashi da matsala Kawai kin tsorata ne da kyawunshi...kar ki kara nuna alaman tsoro in kin ganshi ..kinji ko?..." Ahankali ta kara gyada mata kai don tamkar babbar yaya ta maida asabe yanda Bata yiwa kawo gardama to itama batayi mata gardama.

Yazid na barin factory ya nufi gidan su mufida, daman Tasan da zuwan shi don haka ba karamin haduwa tayi ba don tasha shadda skirt da riga ta gyara kanta sai ta daura dankwali yanda gaban goshinta zai bayyana, har cikin gidansu yayi parking ya fito yayi sallama bakin falinsu, cikin wata irin sexy voice da ya kusa sa shi shivering ta amsa mashi, ahankali ya shigo falon, ita kadaice hakimce kan kujera kaman wata princess, yana ganinta Kawai Al yaji kaman he's should strip her naked an go down with her, dukda yana practicing ustaz yasan over manliness na damunshi cos he easy turns on, wani irin kasaitaccen murmushi suka sakarwa juna,
"Sannu da zuwa baby...nayi missing dinka..." Ta fada mashi in a very low voice kaman tana flirting dashi,
"I miss you too..." Yafada yana zama Dan nesa daita, da Sauri ta mike ta shiga kitchen, sai bin bayanta Kawai yake da kallo yana imagining all this will be his in the next two weeks, mufida irin Matan ne masu kissa don ko bakasonta maganar bakinta Kawai is enough to draw your attention, Sannan she have the perfect body size, medium sized hips same with her boobs ga Iya tafiyan kasaita, tana daga cikin reasons din da yazid bai fiyason zuwa Kano ba cos she always turn him in and yanda ta Iya magana da komai she might not be hard to get most especially yasan no woman can resist him amma alhamdulillah he's not into women, yana cikin tunani ta dawo ta ajiye drink gabanshi
Tana Dana durkushe gabanshi ta daga pure white eyeball dinta ta kalleshi,
"Should I pour the drink?..." Ta tambayeshi cikin whisper, murmushi ya kara sakar mata
"Na hutar dake..." Ya fada mata, ahankali ta mike ta koma ta zauna kan kujera tana tafiya mai dauke hankalin mai kallo, mufida is a gal raised by only female parent after the demise of her multimillionaire father Kuma her mom nada all kinds of friends irin yan duniya nan so the most important thing she learnt was that kana Iya manipulating namiji with kissa and what are view, so hakan yasan she an expert when it comes to handling man's feeling Kuma tana succeeding don her cool and colourful attitude yana daga cikin reasons din dayayi tighting yazid to her
"Ina momcy take..." Ya tambayeta yana bude drink
"Tana upstairs..." Tafada tana Dora kafa daya kan daya,
Tare da zama kan ass dinta daya, tana karkada kafa Ahankali, kara kallonta yayi ta sakar mashi murmushi tana cewa
"Baby yau naga mai kama dai..." Tafada in a low voice, Dariya yayi
"A ina?..."
"A cikin peace TV...."
"Hala majed Mahmoud?..." Yafada yana zuba drink cikin cup, da Sauri tace
"Eh Wallahi.. Baby resemblance dinku is remarkable.. Kaman yan biyu...." Dariya ya karayi yana lumshe idanuwa

"Haka small mom take cewa duk sanda taga program dinshi...ni Kuma ko kadan bana ganin kamanninmu..." Mufida kallon Dan juice da yayi siyaya cikin cup yayi tace
"Yanzu baby Iya Wanda zaka sha kenan?..."
"Yes baby Kawai don kar kayi fushi dani amma small mom ta cika min ciki.. " Bata rai tayi
"Ba dai kana nufin bazakaci abinci a nan ba..." Dariya yayi
"Am sorry.. Gobe nan zanyi dinner..." Bai idaba ta rufe face dinta da left hand dinta ta fara kukan kissa,
"Baby are you crying?.." Ya tambayeta surprisingly,
"Yo sai kace...baka cin ..abinci NA...." Ta fada ciki kuka,
"Ok zan CI...stop crying..." Ya fada mata yana mamakin yanda ta Iya kuka Mara dalili don ko waya suke ba wuya ta fara kuka
"I can't wait inga kina mai dalili..." Yafada cikin ranshi, dauke hannun ta tayi daga face dinta yaga babu hawaye ko daya
"Ko kaifa...." Tafada tana mikewa, Dariya yayi shima ya mike
"Baby babu hawaye fa face dinki...Ashe haka kike yi min ko?... To yau NA ganoki..." Yafada yana biye daita har dinning table,
"Ai don kana nan ne banyi hawaye ba don banason in tada maka hankali..." Tafada tana jawo mashi kujera daya cikin kujerun dinning, zama yayi yana kallon glowing face dinta, abinci ta bude tayi serving dinshi itama tayi serving kanta
"Daman kai nake jira muci abincin..." Tafada mashi. Haka sukaci sukasha sai gyasa yazid yake saboda yanda yayi fulling cikin shi da abinci, sai da yayi sallan magrib a masjid din unguwan su Sannan.
